

# WAKILIN COP

## WAKILIN COP



**Wannan littafi ne dake ƙoƙarin koyar da yara sanin haƙƙinsu da yadda za su kare kansu yayin da su ke amfani da Yanar Gizo. Littafin ya ƙunshi wasu yanayi guda shida (6), waɗanda yara kan tsinci kansu ciki a wannan lokaci na amfani da kimiyar fasahar sadarwa.**

1. **'Yancin da suke dashi na yin wasa a Yanar Gizo.**
2. **Yadda za suyi tattalin lokacin su na wasa a Yanar Gizo.**
3. **Ƙoƙarin horar dasu abubuwan da basu dacewa.**
4. **'Yancin da suke dashi na koyon ilimi ta amfani da fasahar sadarwa ta Yanar Gizo.**
5. **Kare sirrinsu.**
6. **Kare rawar da manya za su iya takawa wajen saita tunanin yara yadda ya dace, wajen yin amfani da Yanar Gizo.**

Kowa ne yanayi da aka kawo cikin wannan littafi yana zuwa wa yara da tambaya ɗaya (1) da kumaamsoshi biyu (2). karanta wannan littafi da 'ya'yanku zai bada dama wajen yi masu bayani game dayadda za su kare kansu yayin da suke amfani da yanar gizo. Amsar da ta yi daidai a kowace tambaya da aka yi, sai a duba ta a bayan littafin.

A yayin da ku ka karanta wannan littafin, muna ƙarfafa maku gwiwa da ku tattauna da 'ya'yanku dangane da abubuwan da suka gani ko su ke yi a yanar gizo. Zai kuma yi kyau idan ku ka ba su tabbaci ko kwarin gwiwar cewa, suna iya tuntuɓarku game da duk wani abu da suka gani a kan yanar gizo, kuma hakan ba zai sa kuyi fushi da su ba.

Wannan littafi an tsara shi ne ga yara waɗanda shekarunsu bai wuce tara ba, don haka kuna iya samun ƙarin bayani dangane da wannan maudu'i a kan adireshinmu na yanar gizo www.itu.int/cop

Ni ne wakilin cop,wayar salula mai matuƙar ƙarfi! Ina zaune a Nijeriya ne da iyalai na, aikina ne na taimakawa yara su ji daɗi tare da basu kariya yayin da suke amfani da yanar gizo, ina so kuma in taimake ku!
Idan har sun saurari abinda Wakilin Cop ya ce cikin littafinsa, to zan taimaka maku wajen nemo amsoshin da suka dace.




**Yauwa abokai na,**
*Yanzu sai mu*
**fara**

# Wannan shi ne OBI





Obi yana wasa ne da
na'ura mai kwakwalwa.
Amma itama 'yar uwarsa
tana son ta yi wasan.

# Me ya kamata Obi ya yi?



**A**

ya faɗa wa ƙaramar ƙanwarsa cewa ba zai yiwu ba?

**B**

Ko itama ƙanwar tasa ta yi wasan, abu ne na jin daɗi, kowa ya more?

## Sai wakilin COP ya ce........

“Dukkan yara na buƙatar su yi wasanni don su ji daɗi”




A yaushe ne ya kamata ku bar ƙananan yara su yi wasanni a kan na'ura mai kwakwalwa?

# Wannan ita ce
# Fatima



Fatima tana ta kallon wasannin cartoon a kowane yammaci, gashi yanzu har idonta ya kumbura.



## Me ya kamata Fatima ta yi yanzu?



A

Ta je wani Shago ta siyo wani sabon idon?

B

Ko kuma ta bar kallon ta yi wasa da ɗan uwanta?

# Wakilin COP ya ce......

"Ai akwai wasanni da dama masu daɗi da za'a iya yi batare da amfani da wayar salula ba, Talabijin ko na'ura mai kwakwalwa."



**Wane wasa ne ku ka fi jin daɗin yin shi da wasu?**

# Wannan shi ne

# TOBI



Tobi yana kallon fasahar sadarwar nan tayara da ake kira da YouTube Kids, kawai sai wani saƙo ya fito daga ciki wanda baya da tabbas a kai.



## Me ya kamata Tobi ya yi a irin wannan hali?



A

Ya kashe na'urar ya gayawa wani babba?

B

Ko kuma ya jefa na'urar cikin shara?

## Wakilin COP ya ce......

"Neman taimakon wani babba zaifi zama daidai wajen samun taimako."

shin wani babba ya kamata a gayawa don neman taimako?



# Wannan ita ce
# DOOSHIMA



Dooshima na son wasan nan na dinosours, don haka take neman ƙarin ilimi a kai.



## Me ya kamata Dooshima ta yi?



**A**

Ta nemo dinosaurs masu rai ta tambaya?

**B**

Ko kuma ta nemi taimakon wani babba da zai nemo mata abubuwan wasanni da ya shafi dinosaur a na'ura mai kwakwalwa.

# Wakilin COP ya ce......




Shin wani shafi yafi burge ka don amfanin yara?

# Wannan ita ce ENIOLA



Eniola na wasanni da na'ura mai kwakwalwa, sai wani abokin wasanta ya ce ta tura masa hotanta.



## Me ya kamata Eniola  tayi?



A

Ta tura hoton wani abokin karantunta?

B

Ko kuma ta tattauna da wani babba?

# Wakilin COP ya ce......




Wane irin babba ne ya kamata a nemi shawararsa game da lokacin da ya kamata a tura da Hoton?

# Wannan shi ne
# ALIYU



Aliyu yana gina wani tsauni mai tsayi,
yana buƙatar  taimakon  mahaifinsa,
saidai mahaifinsa yana wasa da wayar sa?



# Me ya kamata Aliyu ya yi?



**A**

Ya tambayi mahaifinsa cikin hikima su gina tare?

**B**

Ya ji haushi, ya watsar da tubalan ginin a duk inda ya so?

# Wakilin COP ya ce......



## YANAYI NA 1: 'Yancin yin wasa a Yanar Gizo.

Amsarsa ita ce "B"

Dukkan yara na da "Yancin yin wasa, wannan ya haɗa da wasa a yanar gizo, kallon fina-finai, tare da sadar da zumunci tsakanin 'yan uwa da abokan arziƙita kafofin sadarwa da suka dace da shekarunsu.

## YANAYINA 2: DAIDAITA LOKACIN KALLO.

Amsarsa ita ce "B"

Yana da matukar muhimmanci a kula da lafiyar yara tare da daidaita lokacin da suke kallon Talabijin ko na'ura mai kwakwalwa da sauran ayyuka na yau da kullum. Irin waɗannan ayyuka na yau da kullum sun haɗa da wasanni a cikin gida ko waje, karanta littattafai, yin zane-zane ko wasanni na motsa jiki.

## YANAYI NA 3: TSINTAR KAI DA ABUBUWAN DA BASU DACE BA

Amsarsa ita ce A.

Wasu lokutan yara kan tsinci kansu wajen ganin wasu abubuwa da basu dacewa, ko masu bada tsoro, ko tada hankali. Yana da matuƙar muhimmanci yara su fahimci akwai wani amintacce da za su iya tattaunawa dashi game da wani abu daya tayar masu da hankali, dama abun da ya kamata su yi.

## YANAYINA 4: 'YANCIN YIN AMFANI DA FASAHAR SADARWA WAJEN NEMAN ILIMI.

Amsarsa ita ce B.

Babu shakka kowane yaro yana da 'Yancin neman bayanai, sabon ilimi na dabarun sanin makamar aiki dama rayuwa. Fasahar sadarwa ta zamani tana taimakawa a wannan ɓangaren, don akwai shafuka da dama na samar da ilimi da ya zo dashi.

## YANAYI NA 5: 'YANCIN KARE SIRRI

Amsarsa ita ce B.

Yara suna da 'yanci kamar sauran jama'a wajen kare sirrinsu ko bayanai na musamman da ya shafe su, kamar hotuna. Taimako na musamman na taimaka masu wajen samun kariya ga yanar gizo.
wannan nema yasa mafi yawan shafukan sadarwa na yanar gizo ke sanya tsare-tsare da ya shafi kare sirrin masu amfani da shi.

## YANAYI NA 6: RAWAR DA MANYA ZASU IYA TAKAWA WAJEN SAITA TUNANIN YARA GAME DA FASAHAR SADARWA

Amsarsa ita ce A.

Mafi yawan lokuta yara na koyon abubuwa ne daga kallo, don haka ITU ke shawartar iyaye dama manya, da su rinƙa nuna kyawawan ɗabi'u yayin da suke amfani da fasahar sadarwa.
Idan kuna neman ƙarin bayani ITU nada bayanai da zasu iya taimakawa iyaye, malamai da sauran masu ruwa da tsaki. www.itu.int/cop

NIGERIAN COMMUNICATIONS COMMISSION

ITU

*NCC Toll Free Line*: **622**

*Cece Yara Foundation*: **08008008001 (for children, toll free)**

**07007007001 (for adults, non toll free)**

*Email*: ***cop@ncc.gov.ng***

Wannan littafin ba na siyarwa ba ne